# FADAKARWA

## A kan: Kasuwanci da dabarun sai da kaya

## Kashi na 7c: Yadda ake harka da abokan ciniki masu wuyar hali

### Me ya ke sa abokin ciniki ya zama mai wuyar hulda?

Abubuwan da su ke sa abokin ciniki ya zama mai wuyar hurda suna da yawa. Misali abokin ciniki zai iya nuna rashin gamsuwa da dan kasuwa, idan;

- A ka sayar masa da abin da baya bukata.
- A ka sayar masa da abin da bai yaba da ingancinsa ba.
- Ya fahimci an yi masa tsada
- Ya kasa fahimtar yadda za a yi amfani da abin da ya saya
- Ya sayi abu ba tare da bincike ba kafin ya saya.
- Bai sami biyan bukata ba daga abin da ya saya

Ya kamata a lura, sayar da kaya mara kyawu ko kuma al-mundahana/cuta zai iya sa dan kasuwa ya samu riba ta gajeren lokaci ne kawai. Amma daga karshe zai yi da na sani, sabo da abokan ciniki zasu gane kuma su kaurace masa, su daina harka da shi. A tuna cewar mai saye shine Sarki, in ba shi babu kasuwa .

Yayin da mai sayen kaya ya sami rashin gamsuwa:

- Zai ji cewar an yi masa zalunci, kuma an ci amanarsa.
- Zai bata sunan dan kasuwa ta hanyar fadawa jama'a abin da ya faru a gareshi.
- Ba lallai ne ya gaya wa dan kasuwa ba.
- Zai yi wahala a sake jawo hankalinsa.

Sabo da haka dan kasuwa ya kwana da sanin cewar yayin da ya ke da matukar wahala a jawo hankalin sabon abokin ciniki, abu ne mai sauki a rasa wanda a ka saba da shi.

Sabo da haka duk lokacin da abokin ciniki ya zo da wani korafi, ya kamata a nutsu, a saurareshi kuma a dauki matakai kamar haka;

- A saurare shi kuma a amince da abin da ya zo da shi.
- A yi kokarin fahimtar abin da ya haddasa matsalar. Watakila abin ya sami matsala ne wajen ajiya ko sarrafawa daga abokin ciniki.

- A guji doguwar gardama da shi. Idan ya yi fushi , dan kasuwa ne zai yi asara. A nuna masa cewa an fahimce shi sosai, a kuma nemi afuwarsa da faruwar wannan abu.
- A bashi diyya ko da shine ya yi kuskure. Idan kuskuren dan kasuwa ne, to a canza masa wannan abin mai matsala ko a biya shi kudinsa. Idan kuma shi abokin ciniki ya yi kuskuren to ayi masa ragi idan ya yi niyar sayen wani abun.